## ABOUT CITAD

CITAD (www.citad.org)
Is A Capacity Building Civil Society Organization
Whose Activities Covers Research, Advocacy,
Training And Publicity In All Areas Of Icts.
Its Vision Is; A Knowledge-based Democratic Society
Free Of Hunger While Its
Mission Is; Using ICTs To Empower Citizens For
A Just And Knowledge-based Society
That Is Anchored On Sustainable
And Balanced Development.

**MAIN OFFICE:**
3rd Floor, NISTF Building, No.1A, Social
Insurance Road, Behind Trade Fair Complex,
Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 0800-68078282, 080-54362931, 070-33427467 •
E-mail: info@citad.org, Citadev@gmail.com, citad4peace@citad.org,
Website: www.citad.org, www.citad4peace.org.ng

**BAUCHI OFFICE:**
NUJ Secretariat, Opposite Reinsurance House,
Ahmadu Bello Way, Bauchi State.
GSM: 08064867312

**CITAD**.....*A Knowledge-Based Democratic Society Free of Hunger*

*Tsarawar*
Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)
Tare Da
Gudummawar ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)

# KUNDIN SAMAR DA CIGABAN KARAYE-GARI



CENTRE FOR INFORMATION TECHNOLOGY AND DEVELOPMENT

# KUNDIN SAMAR DA TSARIN CI GABAN ƘARAYE-GARI

*Tsarawar*

**Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)**
**Tare Da**
**Gudummawar Ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)**

CITAD actionaid UKaid from the British people





## ABUBUWAN DA KE CIKI


Shafin Farko....................i
Jadawali....................ii
Godiya....................1
Gabatarwa....................2
Manufa....................3
Hanyoyin Da Aka Yi Amfani Da Su....................3
Tsarin Da Aka Yi Amfani Da Shi....................3/4
Cikakken Bayani Game Da Karaye-Gari....................4/7
Kadarori....................7/8
Tarihin Karaye-Gari....................8/9
Taswirar Karaye-Gari....................9/10
Yanayin Zamantakewa....................12
Arziƙin Da Allah Ya Huwacewa Garin Karaye....................12/16
Lafiya....................16
Ilimi....................16/17
Juyawar Yanayi....................18
Jadawalin Juyawar Yanayi Na Tsahon Shekara....................18/20
Kadarori....................20
Tantance Matsalolin Da Ke Addabar Karaye-Gari....................21
Tantance Haƙƙoƙin Mata....................21/23
Jadawali Ayyukan Yau Da Kullun....................24/25
Take Haƙƙoƙin Ɗan Adam....................26/27
Kalubalen Da Ke Fuskantar Karaye-Gari A Halin Yanzu....................28/30
Sassauƙar Hanyar Jera Matsaloli2....................30/32
Tantance Matsaloli Ta Amfani Da Bishiyar Matsaloli....................33/34
Jadawalin Tantance Matsaloli Karaye-Gari....................35
Tantance Yanayin Karfin Iko (Nazari Kan Waɗanda Keda Iko).......... 36/37
Tantance Hanyoyin Samun Bayanai....................37/38
Tsarin Da Aka Shirya Gudanarwa Na Al`Umar Karaye-Gari....................39/40
Hotunan Da Akayi Amfani Dasu Wajen Sassauƙar Hanyar Jera Matsaloli.......
....................41/42

# GODIYA

Wallafawar wannan littafi yasamu yiwuwane tareda tallafi daga Sashin Kula da Cigaba na ƙasa da ƙasa na Gwamnatin Birtaniyya (DFID ta hannun ƙungiyar ActionAid Nigeria (AAN). Dole ne a yabawa wannan Cibiya ta ActionAid saboda jajircewa ta wajen Bunƙasa Demokuraɗiyya ta hanyar wayar da Jama'a su fahimci Demokuraɗiya.

Muna godiya ta musamman ga Shugaban Cibiyar Fasahar Sadarwa da Ci gaban Al'umma (CITAD), Y.Z. Ya'u domin kasancewarsa jigo wanda ya bada gudummawa ga kammaluwar wannan Littafi.

Godiyar mu bazata cikaba sai mun yaba da Kyakkyawar fahimta da hadin kai da ma'aikatan CITAD. Haka kuma mun yabawa da ƙoƙari da himmar Malam Ahmad AbdullahiYakasai, da Isyaku Garba' da Abubakar Auyo da Mukhtar Sulaiman Umar da Abdullahi Jido da Harira Abdulrahman wanda suka hana kansu hutu domin tabbatar da kammaluwar wannan Kundi.

Muna miƙa cikakkiyar godiyarmu ga 'Yan kwamitin aiwatar da kundin wannan Gari na Karaye-Gari da Mai Gari da Dagaci da kuma dukkannin waɗan da suka tallafa wajen gudanar da tsarin shirin wannan kundi, babu shakka zai ingan ta shirin nan gaba.



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN ƘARAYE-GARI 2016

# GABATARWA

Wannan kundi na cigaban wannan gari yana ɗauke da taƙaitattun bayanai game da Karaye-Gari. An tattaro waɗannan bayanai ne ta hanyar yin amfani da tsarin waiwaye adon tafiya da kuma sabon tsarin nan na CITAD/ActionAid wanda ke bai wa kowa damar bayar da gudummawarsa. Wannan tsarin ginshiƙi ne na aikin CITAD/ActionAid da al'umma a mataki na gaba. An samar da kundin ne ta bin managartan tsare-tsare da wannan ƙungiya ta yi a baya, aka tattaro ƙwararru suka yi aiki ƙarƙashin inuwa ɗaya. Hanyar amfani da tsarin waiwaye adon tafiya na yin amfani da cikakken bincike game da mutanen da ke rayuwa cikin talauci ta ɗaya daga cikin waɗanan hanyoyin: Binciko dangantakar mahukunta da haƙƙoƙin al'umma musamman mata da gano abubuwan da ke yi wa garin barazana da binciko ƙungiyoyi da mutanen da za su iya tallafawa da fahimtar hanyoyin sadarwa da al'ummar garin ke amfani da su da kuma matsalolin da suke ci musu tuwo a ƙwarya.

Domin cimma nasara abubuwan da aka ambata a Sama, CITAD ta aiwatar da tsarin waiwaye adon tafiya a Karaye-Gari cikin Karamar Hukumar Karaye ta Jihar Kano. Bayanan da aka tattara a ƙarƙashin wannan tsarin za suyi amfani domin Zama ginshiƙai na ƙarfafa gwiwa wanda zai ciyar da garin gaba yadda ake buƙata.

MANUFA

Manyan manufofin wannan kundi su ne kamar haka:

- Gabatar da bayanai game da Karaye-Gari wanda zasu taimaka wajen ragewa jama'a raɗaɗin talauci da abubuwan da ke yiwa ɗaiɗaikun al'ummar garin tarnaƙi dama iyalai gabakiɗaya ya kuma samar da cigaban garin.
- Tallata ƙwarewa da ilimi da kuma abubuwa da Karaye-Gari ke fatan samu a dunƙule domin samun sauƙin bibiya.

MANUFOFIN TSARIN WAIWAYE ADON TAFIYA

- Tattara bayanan sakamakon da aka samu dangani da manufofin shirin CITAD/ Actionaid
- Tattara sahihan bayanan Karaye-Gari wanɗanda zasu iya zama sanadiyar cigaban garin.

HANYOYIN DA AKA YI AMFANI DA SU

Hanyoyin da aka bi wajen aiwatar da aikin sun haɗa da:

- Ziyarce-Ziyarce: An ziyarci wurare daban-daban tare da ganawa da mutanen gari na tsawon kwanaki 3 domin samun cikakkun bayanai na ɓangarorin nan bakwai na Reflection Action.
- Tattaunawa tun a karon fari tsakanin dattawan Karaye-Gari da CITAD.
- Taron tantancewa da rubuta rahoton abubuwan da aka gano.

TSARIN DA AKA YI AMFANI DA SHI

An yi amfani da abubuwa daban-daban wajen tantance ɓangarori nan bakwai na waiwaye adon tafiya wato Reflection Action.

An yi amfani da taswira wajen binciko matsalolin da ke addabar garin.

An yi amfani da jerin gwanon haƙƙoƙi ɗan Adam wajen gano haƙƙoƙin al'ummar Karaye-Gari.

Jera abubuwa mafi sauƙi ya taimaka wajen tsara al'amuran da suka fi muhimmanci bi da bi waɗanda al'ummar garin suka gano.

An yi amfani da bishiyar-matsaloli domin fahimtar abubuwan da suka haddasa matsalolin da tasirinsu da kuma tattaunawa mai zurfi a kansu.





An yi amfani da salon tantance cibiyoyi da mutanen da za su iya bayar da tallafi domin gano waɗanda za su iya hoɓɓasa kuma suke da ikon kawo canji ga abubuwan da garin ke buƙata.

An yi amfani da tsarin zane na Ɓenn domin a tantance matakin tasirin da cibiyoyi da mutanen da za su iya taimakawa da alaƙarsu da garin.

An yi amfani da salon yanar-gizo wajen tantance haƙƙin mata.

Tsarin tantance matsaloli ya fitar da abubuwa daban-daban da ka iya cutar da garin.

Zanen hanyoyin sadarwa ya tantance hanyoyin da al'ummar garin ke isar da saƙonni tsakaninsu da sauran garuruwa da waɗanda za su iya bayar da gudummawa. A ƙoƙarin aiwatar da tantance abubuwa daban-daban, antattauna da kowa da kowa, an tattauna a ƙungiyance don a yi tambayoyi da kuma yin bincike mai zurfi domin a samu tantancewa mai inganci.

CIKAKKEN BAYANI GAME DA KARAYE-GARI

| | |
|---|---|
| Sunan Garin: | Karaye-Gari |
| Karamar Hukuma: | Karaye |
| Jiha: | Kano |
| Adadin Al'umma: | 22,500(Maza: 10,000, Mata12,500) |
| Adadin ƙiyasin Magidantan Garin: | 10,000 |
| Adadin Dattijai daga cikin Magidanta: | 3,000 |
| Adadin Mata Magidanta: | 600 |
| Adadin Matasan Magidanta: | 200 |

Jadawali na 1Ajujuwan Shekarun Al'ummar Garin

| AJUJUWAN SHEKARU | KIYASI |
|---|---|
| Shekara 0 zuwa 5: | 2,500 |
| Shekara 6 zuwa 10: | 3,000 |
| Shekara 11 zuwa 18: | 3,000 |
| Shekara 19 zuwa 30: | 4,000 |
| Shekara 31 zuwa 40: | 3,000 |
| Shekara 41 zuwa 50: | 4,000 |
| Shekara 51 zuwa 60: | 2,000 |
| Shekara 61 zuwa 70: | 800 |
| Shekara 70 zuwa sama: | 200 |
| Adadin Al'ummar Gabaɗaya:= | 22,500 |

Kiyasin Na Mahalarta Taron Samar Da Kundi Ne (2015) Daga Cikin 141,407 Kidayar 2006

MADOGARA: ɗaya daga cikin mahalarta taron samar da kundin cigaban garin

SANA'OI /AIKIN YI: Noma (Noman Hatsi), Kiwon Shanu, Kasuwanci (Yan tireda) da Ma'aikatan Gwamnati.
KAYAYYAKIN ABINCIN DA AKE NOMAWA A GARIN: Gero, Dawa, Wake, Masara, Gyaɗa da Kayan Miya.
KUƊAƊEN DA KE SHIGOWA/KUƊAƊEN DA AKE KASHEWA
Matsakaicin abin da ke shigowa mutum a shekara: N 500,000
Matsakaicin abin da mutum yake kashewa a shekara:N 400,000
Matsakaicin abin da ma'aikaci yake samu a shekara: N 500, 000
Matsakaicin abin da ma'aikaci yake kashewa a shekara: N500, 000
KUƊAƊEN DA KE SHIGOWA
ADADIN MUTANEN DA SUKA MALLAKI GONAKI DA KANANAN SANA'O'I: Kowanne magidanci kan mallaki gonaki.
ADADIN MATAN DA SUKA MALLAKI GONAKI DA KANANAN SANA'O'I: Ɗaukacin matan garin kan shiga a dama dasu wajen ɗaya daga cikin sana'o'in dake akwai a garin. Yawancinsu kanyi kiwon dabbobi kamar Awaki, Tumaki da Kaji.Haka kuma ƙalilan daga cikinsu sun mallaki Shanu.





| JADAWALI NA 2 LAFIYA |
|---|
| Ɗakin Shan Magani:Gwargwadon nisan ɗakin shan magani da al'umma ƙasa da kilomita daya ne. wato a cikin gari yake, kuma ance ana da ƙwararrun ma'aikatan lafiya sama da 5 ke da akwai a ɗakin shan maganin wanda koyaushe akan samesu a ɗakin shan maganin. 3 daga cikin ma'aikatan maza ne 2 kuma mata. Ana karba haihuwa. |
| Idan aka sami ɓarkewar annoba ana warware matsalar ta hanyar kulawa da marasa lafiya da keɓance su daga cikin mutane da kuma basu shawarwari. Kalilan daga cikin matan garin kan haihu a ɗakin shan magani garin. Idan haihuwar da tazo da matsala, akan tura mata babban asibitin garin Gwarzo domin shawo kan lamarin |
| Cigaba ta abubuwan da suka shafi lafiya, kawo yanzu zuwa shekaru uku baya babu wani cigaban azo a gani da aka samu a harkokin lafiya a wannan gari. |

**ILIMI**
Makarantu: Akwai makarantu gwamnati da waɗanda al'umma suka samar da dama a wannan garin. Akwai makarantu biyar na koyon sana'o'i (huɗu ta maza ɗaya kuma ta mata) da kuma sabuwar makarantar mata da aka buɗe a shekarar 2010.

ADADIN YARAN DA SUKA SHIGA MAKARANTA A HALIN YANZU
Adadin yaran da suka shiga makaranta a Karaye-Gari
Adadin yara 'yan shekaru 6 zuwa 11 (maza: 14, 097 mata: 13,174 Jumulla: 27,270)
Adadin yara 'yan shekaru 12 zuwa 14 (maza: 6,040 mata: 5,091 Jumulla: 11, 131)

| Firamare | | | Karamar Sikandire | | |
|---|---|---|---|---|---|
| Maza | Mata | Jumulla a tsakaice | Maza | Mata | Jumulla |
| 112 | 100 | 106 | 48 | 15 | 33 |
| Adadin waɗanda suka kammala firamare a garin: 1148 | | | Adadin Maza:596 | | |
| | | | Adadin Mata:558 | | |
| Adadin waɗanda suka kammala sakandare a garin:2200 | | | Adadin Maza:1135 | | |
| | | | Adadin Mata:1065 | | |
| Adadin waɗanda suka kammala makarantar gaba da sakandare a garin:1100 | | | Adadin Maza:1089 | | |
| | | | Adadin Mata:1019 | | |
| Adadin waɗanda ba su taɓa zuwa makaranta ba: 1150 | | | Adadin Maza:550 | | |
| | | | Adadin Mata:600 | | |

Madogara: Ɗaya Daga Cikin Mahalarta Taron Samar Da Kundin Cigaban Karaye-Gari, 2015

## KADARORI

Adadin matan da suka mallaki filaye/gonaki: babu wani takamemen ƙiyasin matan da suka mallaki filaye ko gonaki, sai dai jama'ar garin sun bayyana cewa mata na da cikakken ikon mallakar kadarori a garin. Da yawa daga cikin matan sun mallaki gonaki da dabbobi.

JADAWALI NA 4: KADARORI

| | | | |
|---|---|---|---|
| Kadarori (ƙiyasi) | Kiyasin adadin waɗanda suka mallaki gonaki da ƙananan yan kasuwa15,000 | Sama kaso 60 cikin 100 sun mallaki gonaki da ƙananan sana'o'i | Adadin matan da suka mallaki gona da ƙananan sana'o'i 4,000 |
| Masu buƙata ta musamman | Adadin yawan masu buƙata ta musamman: 21(ƙiyasi) | Adadin maza masu buƙata ta musamman: 15 (ƙiyasi) | Adadin mata masu buƙata ta musamman: 6 |





JADAWALI NA 5: Juyawar Yanayi

| JUJJUYAWAR YANAYI | | | |
|---|---|---|---|
| Samun ruwan sama ya kai mizanin 42.8 digiri a ma'aunin samun ruwan sama | Lukutan samun ruwan sama ( watanni) Watanni 6 | Tsahon lokacin samun ruwan sama (a watanni) wata 6 | Tsahon lokacin samun ruwan sama (a watanni) wata 6 |



## TARIHIN ƘARAYE-GARI

Karaye-Gari shi ne garin da yafi kowanne girma a cikin Karamar Hukumar Karaye, haka kuma nanne shedikwatar Karamar Hukumar ta Karaye tun watan Mayun shekarar 1989. Garin nada nisan 90km yamma daga Kano. Haka kuma garin nada adadin yawan al'umma kusan 144,075 kamar yadda jadawalin ƙidayar shekarar 2006 ya nuna cikinmasarautar garin da ta ƙunshi garuruwa sha bakwai wanda suke ƙarƙashin kulawar hakimin Karaye (Sarkin Karaye) a masarautar Kano.

Al'ummar garin Karaye Hausa Fulani ne, waɗanda suka ƙware wajen tarairayar jama'a da ƙabilu daban-daban daga duk inda suke ba tare da nuna ƙyama ba.Shahararrun sana'o'in al'ummar garin shi ne noma da kasuwanci.Kayayyakin da suka fi siyarwa sun haɗa da kifi, shanu da hatsi (masara, dawa, gero, wake da shinkafa).

Kamar dai garin Mesopotamia da yake tsakanin koguna guda biyu, kogin Tegris dana Euphrates, garin na Karaye na tsakanin wasu manya Dama-Dame guda biyu (Dam ɗin Challawa Goje da Kusalla Dam). Jama'ar yankin na amfanin da waɗannan Dama-Daman wajen noman rani inda suke noman tumatir da sauran kayan miya. Haka kuma suna mutuƙar amfanuwa da waɗanan sana'o'in ƙware da gaske.

Akwai tarihin wata masarauta da aka gina lokacin Jihadin Fulani, Jihadin Shehu Usman Ɗan Fodiyo, wadda sarkin Karaye na farko Sarki Sulaiman Ndoji ya gina. Daɗaɗɗen tarihin masarautar da ta samar da dubunnan Mayaƙa Mahaya doki domin tsaro da tunkarar duk mayaƙan da suka kawo hari ta yammacin ƙasar Kano. Haka kuma, a yanzu haka akwai bikin sallar da akeyi duk shekara wanda ɗaruruwan mahaya doki ke baje al'adu daban-daban. Shahararren dutsen nan Dutsen-Amare dake da nisan kilomita 3 arewa daga garin ya ƙarawa garin ado da ƙaye. Garin na ƙaraye na da kasuwanni dake ci mako-mako waɗanda ke jan hankalin 'yan kasuwa daga guraren daban-daban.Misali, daga maƙotan jihohin Katsina da Kaduna.'Yan kasuwar kan gudanar da kasuwancin su hankali kwance. Allah ya albarkaci garin na Karaye da ma'adanai iri daban-daban kamar ma'adanin FELDSPAR, KUARTZ, GRANITE, MICA, da sauran duwatsu masu daraja kamar Allubial Gold, Sapphire, Emeralds da Tourmaline waɗanda ake ɗibansu da izinin hukuma domin siyarwa a ƙasashen waje.

## **TASWIRAR** KARAYE-GARI

Samar da taswirar ya soma ne da tattaki cikin ƙwaryar garin. Tattakin ya bayar da damar samun gamsassun bayani game da garin, matsaloli da damarmakin dake akwai a garin. Muhimman abubuwan da aka gano sun haɗa da ababan more rayuwa, albarkatun ƙasa. Taswirar ta nuna yadda garin yake a yanzu da kuma irin canje-canje da garin ke son cimmawa a gaba. Taswirar ta kuma nuna guraren da suka haɗa da gidaje, makaranta, masallaci, ɗakunan shan magani, kasuwa, rijiyoyi a duk inda suke a cikin garin



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN ƘARAYE-GARI 2016





Figure 1: Taswirar Karaye I


Figure 1: Taswirar Karaye II UGUWAR HAJJI



Jama'ar Garin Ke Tattaunawa Lokacin Samar Da Tasawirar Yankin



YANAYIN ZAMANTAKEWA

Al'ummar Karaye-Gari yawancinsu manoman hatsi ne. Matsakaicin abin da ke shigowa mutum magidanci a shekarashi ne ƙiyasin N500,000.Haka kuma matsakaicin abinda mutum magidanci ke kashewa a Shekara yakai ƙiyasin N 550,000 (Matsakaicin abin da ke shigowa mutum magidanci a kullum yakai N550)(matsakaicin abinda Mutum magidanci ke kashewa a kullum yakai N550). A wani gefen kuma, Matsakaicin abin da ma'aikaci ke samu a shekara shi ne N400,000 sannan kuma matsakaicin abin da ma'aikaci ke kashewa a shekara shi ne N400, 000





ARZIKIN DA ALLAH YA HUWACEWA GARIN KARAYE KASAR NOMA

Al'ummar wannan gari na mutuƙar alfahari da ƙasar noman da suke da ita a wannan yanki, saboda albarkacin noman da ƙasar gurin ke da ita tasa ɗaukacin al'ummar yankin zama manoma tun da can. Akwai wajajen da aka ware saboda noman rani a tsahon shekara gabaɗaya, wajajen sun haɗa da ƙauyukan Maa, Daura, Turawa da Tudun-Kaya, inda ake noman Rake da Tumatur da dama. Zai yi mutuƙar fa'ida idan masu saka jari zasu zo su saka jarinsu a wannan yankin domin cin moriyar kayayyakin da ake nomawa a wannan guri.

MA'ADANAI

Allah ya albarkaci wannan Karamar Hukuma da ma'adanai da dama kamar su FELDSPAR, MICA, GRANITE, KUARTZ da sauran duwatsu masu daraja (Tourmaline, Emerald, Alluɓial Gold da SAPPHIRE).An bayyana dutsen Feldspar a matsayin dutsen da aka fi samu da yawa a yankin. Ana amfani da shi wajen yin Gilasai a masana'antun da suke samar da kayan ƙarau kamar Kwalabe, Tambulan Shan Ruwa, Kayan Kwaliyya 'Yan China, Tayal Ɗin Kasa da na Bango da sauran abubuwa da dama. Ga kuma:

GURAREN YAWON BUƊE IDO

- Fadar Sarkin Karaye
- Dam Ɗin Challawa Goje (Mafi girma a Afirka)
- Ruwan Baturiya
- Kogunan Dutse Masu Ban Tsoro Kamar Kogon Damisa
- Dutsen Amare
- Dam Ɗin Kusalla (Inda Ake Bikin Kamun Kifi da Horas da Yara Masu Bautar Kasa)
- Kwazazzabon 'Yarkwando

Mazauna gurin na asali su suka sawa kogin suna Challawa wanda yake nufin “TINJIN” sunan ya samo ne daga irin ƙarar da ruwan kogin keyi idan yana tafiya musamman lokutan damina idan ruwa ya kawo. Yawanci kogin yana tafiya ne tsakanin duwatsu biyu yai gabas har zuwa kogin Haɗeja da na Jama'are.

Kogin shi yafi kowanne kogi girma a faɗin Afrika wanda aka gina na zamani, yanada tsahon kilomita 7.8 da kuma zurfin 527.5 daga saman ruwa. Haka kuma kogin nada faɗin mita 42.

Dangane da abin da ya shafi Ma'adanar ruwa ta kogin kuwa, girmanta yakai 930m ko kuma 6.20cm.Dam ɗin ya mamaye kusan hekta 40,000 na ƙasa, wanda zai yi kyau wajen samar da filin wasanni da wajen shaƙatawa kamar wasan ƙwallon rami da lambunan hutawa.

A ƙarshen shekarar 1970 ne akayi shawarar gina Dam ɗin Challawa Goje, inda gwamnan Kano na wancan lokacin ya karɓi shawarar ya kuma danƙa aikin ginin Dam ɗin ga Kamfanin Ruwa na gwamnatin Jiha wato WRECA. (Water Resources and Engineering Construction Agency). Duk da cewar sunyi iya ƙoƙarinsu wajen tafiyar da aikin yadda yakamata, sun sami tasgaron kuɗi dana dokar da zasu taimaka wajen kammala aikin yadda ake buƙata. Daga ƙarshe, Sarkin Kano Alhaji Dr. Ado Bayero ya roƙi Shugaban Kasa Janar Ibrahim Badamasi Babangida don cigaba da aikin. Wannan tasa gwamnatin tarayya ta ɗauki gabarar tafiyar da aikin gabaɗayansa. Ta danƙa aikin ga kamfanin gini na Juliyos Baga (Julius Berger) don kamala shi, gwamnati kuma ta ƙaddamar dashi. Yanzu haka Dam ɗin na ƙarƙashin kulawar Ma'aikatar Ruwa ta Gwamnati Tarayya.

## IDANIYAR RUWAN DUTSE

Ziyartar wajen zai yi mutuƙar bada sha'awa,ganin yadda ruwa ke ɓuɓɓugowa daga Dutse. Kamfanin Julius Berger da sukayi aikin gina Dam ɗin sun yi ƙoƙarin keɓe wajen domin amfani dashi. Suka gina wata madatsar ruwa domin sarrafa gudanar ruwan. Saboda daɗin ɗanɗanon ruwa ake kiransa da suna RUWAN YANKARI ko kuma RUWAN BATURIYA yadda yake ɗaukar hankalin 'yan yawon buɗe ido. Gurin na nan kusa da mabuɗar ruwan Challawa Goje Dam idan ka taho kusa da gada kan titin Karaye zuwa ƙauyen Turawa.





Ɓuɓɓugowar da ruwan keyi,yasa kamfaninnika sayar da ruwan roba amfani da gurin kamar kamfanin Ɗan Karaye, Getso Pure Water da sauransu.

## KOGUNAN GIDAJEN TURAWA (A KAUYEN TURAWA)

Abin mamaki baya ƙarewa, waɗansu wuraren ƙayatarwa a garin na Karaye sun haɗa da sanannun wuraren nan da suka haɗa da Ramin Yaburbura, Dutsen Kura da Kogon Damisa.

## KOGON YABURBURA

Kogon Yaburbura shi ne inda zaka fara gani a ƙauyen Turawa. Kogon na nan daura da Ruwan Baturiya. Mutuƙar an sako ruwa daga madatsarsa yana yiyowa gabas ƙasan kogon. An ce waɗannan tsuntsayen sunyi shekaru dubunnai suna zama cikin wannan kogon. Tun daga nan ake kiran wannan kogo da suna "Ramun Yaburbura". Kogo ne dake da tsahon mita 25 da kuma zurfin mita 2.5. Mashigar Kogon tayi kewaye, tayi faɗi daga farko daga ƙarshe kuma a tsuke take. Ta fara daga kudu tayi arewa. Har yanzu zaka sami irin waɗannan tsuntsayen a cikin Kogon, tsuntsayen basa cutar da kowa saboda sabon da suka yi da jama'a.

## DUTSEN KURA DA KOGON DAMISA

Kana wucewa ta ƙauyen Turawa akwai tsaunika guda biyu daura da juna daga Kudu maso Gabas da ƙauyen. Guda daga ciki tsaunin gurin zama ne na Kuraye inda ake kiransa da suna Dutsen Kura. Haka Damisu ke zama a ɗaya tsaunin da ake kira da suna Kogon Damisa. Kamar yadda mazauna gurin suka tabbatar, Damisun ke cinye musu Tumakai da Awakai.Su kuma Kurayen ke kashe tare da cinye musu Karnuka. Waɗannan Koguna har yanzu kaniyazamawajen yawon buɗe ido, amma Kurayen da Damisun tun shekaru arba'in baya aka koresu daga gurin.

## DUTSEN AMARE

Nan kuma wani guri ne mai ban ƙaye wanda aka fi sani da -

suna Dutsen Amare, mai nisan kilomita 3 arewa daga garin Karaye. Rukunin duwatsu ne mabanbanta guda tara a jere daga yamma zuwa gabas. Ana da yaƙinin cewa duwatsun mutane ne suka canza suka koma duwatsu a siffar amarya wadda ta taho daga gidan iyayenta zuwa gidan mijinta.Katsahan ita da 'yan rakiyar tata suka koma duwatsu. Lamarin ya faru ne saboda ansa addu'ar amaryar da Allah Maɗaukakin Sarki yayi akan hakan ta kasance. An Ambato cewa tawagar amaryar suna kan hanyar tasu ne yayinda suka tsinkayi wasu tawagar mahara suna tunkaro su, sai suka miƙa lamarinsu ga Allah suka roƙeShi ya mayar dasu duwatsu. An bawa ɗaukacin duwatsun tara sunayen da zasu dace da tawagarAmaryar da jeren 'yan rikiyarta yadda su taho. Sunayen kuwa su ne: Amarya, Gunki, Ɓauraina, Tsamiya, Fyaɗi, Shato, Nalare, Baja da Ungulu, za a sami duwatsun a jere ɗaya bayan ɗaya. Zai yi mutuƙar ban ƙaye ga masu ziyartar wajen.

DAM ƊIN KUSALLA

Gwamnatin Jihar Kano ceta gina wannan Dam ɗin tare da sanannan wajen noman ranin nan na Kadawa a shekarar 1970. Dam ɗin na bawa ƙananan hukumomi huɗu ruwan sha, ƙananan hukumomin kuwa su ne: Karaye, Gwarzo, Shanono da Kiru. A geffan Dam ɗin kuwa ayyukan noman ranine ke gudana.

Kawowa yau,yana cikin kundun tarihin jiha bikin kamun kifin da Ma'akatar Yawon Buɗe Idanu ta Jiha tare da haɗin guiwar Karamar Hukumar Karaye suka shirya a shekarar 1998 wanda yaja hankalin 'yan yawon buɗe ido da dama. Hikimar ita ce jan hankalin al'umma kan alfanun dake tattare da Dam ɗin.

A yanzu haka, wurin da aka tanada domin horas da 'Yan Bautar Kasar da aka turo jihar Kano a gabas da Dam ɗin yake wanda zai iya ɗaukar dubunnan Samarin 'Yan Bautar Kasa waɗanda suka kammala Jami'a a ɗaukacin ƙasa Najeria dama waje.





KWAZAZZABAN 'YARKWANDO

Kwazazzabon na nan kilomita 20 gabas da garin Karaye, yayi iyaka da Kananan Hukumomin Kabo da Kiru. Kamar yadda tarihi ya nuna, a wajen ne Fulanin da suka taho Jihadi sukayi sansani da nufin tunɓuke masarautar Kano da Karaye domin tabbatar da mulkin musuluncin da Daular Shehu Usman Ɗanfodiyo dake Sokoto ta ɗabbaƙa a shekarar 1804. Gurin nada mutuƙar muhinmanci inda akeyi la'akari da tarihin da ya ƙunsa.




## LAFIYA

Asibitin (Ɗakin shan magani) guda ɗaya ake dashi a garin wanda gwamnati ta gina. asibitin na da ma'aikata 12 daga cikinsu 5 maza ne sauran 7 kuma Mata ne.

Gudummawar da Ɗakin Shan Maganike bayarwa ga jama'ar gari tana buƙatar kawo tallafi. Mutanen wannan garin kanyi tafiyar misalin kilomita 5 - 6 zuwa babban asibitin Karamar Hukumar Gwarzo domin samun ingantancciyar kulawa dangani da abin da ya shafi lafiyarsu. Hakan ba ƙaramar wahala ke jawowa marasa lafiyar ba musamman mata masu juna biyu.




## ILIMI

Akwai makarantar firamare guda ɗaya a cikin garin, makarantar na ɗauke da rukunin ginin ajujuwa 12, rukunin ginin wadda gwamnati ta gina na ɗauke da ajujuwa sama da 30. Adadin yaran da suka shiga makaranta a halin yanzu na ƙunshe a jadawali na 3 a sama. Jadawalin yayi ƙarin haske kan adadin yara maza da mata da suka shiga makaranta a halin yanzu.Dama iri ɗaya ake bawa mata wajen samun ilimi da yan uwansu maza.Hakan kuwa ya faru ne sakamakon irin gudunmowar da wasu dattijan garin ke bayarwa.Akwai mutane da dama masu ilimin addini dana zamani a garin na Karaye. Ko kafin wannan yunƙurin, adadin mata da ake

ɗauka a makarantu a garin Karaye nada dama. Anyi amfani da Shirin bunƙasa damar samun ilimi PRS domin tantance inganci ilimi a Karaye-Gari.Shirin bunƙasa damar samun ilimi PRS ya fayyace haƙƙoƙi guda 10 da aka samu daga dokokin ƙasa misali anyi amfani da kundin tsarin mulkin ƙasa da tarukan kare haƙin ɗan adam wajen tantance ingancin ilimi a Karaye-Gari.


Babbar manifar wannan shiri na PRS shine shigar da yan ƙasa cikin tsarin bunƙasa ilimi. Anyi amfani da kundin wajen tantance mizanin fahimtar damar samun ilimi musamman ta fuskar al`umar wannan gari su san cewar damar su ce. Tare da mizani mai lamba 1 mafi ƙaranci da lamba 5 mafi girma. Jadawalin da ke tafe yayi ƙarin haske




Jadawali na sama ya nuna cewa jama'a basa shiga a dama da su a wajen ɗaukar mataki kan wani abu da ya shafi al'umma. Haka kuma ga isassun kayayyakin more rayuwa, amma kuma an tauye musu haƙƙin samar musu da ingantacciyar koyarwa.








## JUYAWAR YANAYI

Karaye-Gari nada yanayi iri biyu, rani da damina. Ana samun damina yawanci tsakanin watannin Afrilu da Satumba, shi kuma lokacin ranin na zuwa ne tsakanin watannin Oktoba da Maris. Jama'ar wannan gari na samun ruwan da suke amfani dashi yau da kullum mafi kusa ta fanfon tuƙa-tuƙa da kuma rijiyoyi a cikin garin.

Jadawalin da ke tafe zai taimaka mana mu fahimmaci ayyukan da aka fi yi tsahon shekara a wannan gari.

JADAWALIN JUYAWAR YANAYI NA TSAHON SHEKARA




Karin haske: ƁHSama da Gaske  H  Sama  M Matsakaici  L  Kasa ƁL  Kasa Sosai



Jama'ar Garin Wajen Samar Da Jadawalin Jujjuyawar Yanayi A Tsahon Shekara



Jama'ar Karaye-Gari Wajen Samar Da Kundin Cigaban Garin







Jama'ar Karaye-Gari Wajen Samar Da Kundin Cigaban Garin





## KADARORI

Ɗaukacin magidanta a garin nada gona ko ƙananan sana'o'i. Mazan garin sunfi yin ayyukan noma akan 'yan uwansu mata, sai dai babu wani takamemen ƙiyasi akan adadin maza ko matan da suka fi yawa akan abin da ya shafi kasuwanci a garin, amma tattaunawar da akayi da mambobin samar da kundin ya nuna cewa maza sun fi 'yan uwansu mata sana'o'i da kasuwanci. Du ɗan garin na iya mallakar gona ko kiwon shanu ko sauran ƙananan sana'o'i kamar yan tireda, yin man girki. Haka kuma, matan garin kan mallaki dabbobi (Awaki da Tumaki) da yin sana'ar sayarda Daddawa da mangyaɗa da sauran kayayyakin miya.




## TANTANCE MATSALOLIN DAKE ADDABAR ƘARAYE-GARI

Al'ummar wannan garin su bayyana waɗannan Al'ummar wannan garin su bayyana waɗannan matsalolin a matsayin matsalolin da suke addabarsu. Matsalolin su ne: shan miyagun ƙwayoyi da rashin Aikinyi ga matasan gari. Waɗannan manyan matsaloli ne wanda mutuƙar dai ba a magance su ba akan lokaci, zasu haifar da ƙaruwar taɓarɓarewa tarbiya da sauran laifuffuka a cikin al'umma.



VULNERABILITY ANALYSIS OF KARAYE UNGUWAR HAJI / [illegible]

| HAZARD | ROOT CAUSE | IMPACT / EFFECT | MOST VULNERABLE |
|---|---|---|---|
| Conflict between farmers and cattle rearers | Farm product | lost of lives and properties | Youth & Farmers |
| Maleria | poor sanitary environment | Lost of lives | Children |
| Meseals | Poor environmental sanitation | Lost of lives | Children |




## TANTANCE HAKKOKIN MATA

'Yancin mata shi ne haƙƙoƙinda aka keɓe musamman domin mata da 'yanmata a ƙasashen duniya masu yawa.A wasu wuraren, ire-iren Waɗannan haƙƙoƙinana tabbatar da Su ne ta hanyar yi musu doka da tsarin zamantakewar al'umma. A wasu wuraren kuwa, a iya cewa an yi watsi da su. Lamuran da ake dangantawa da haƙƙin mata ba a takaita su ga 'yancin yin zabe ko takaita haihuwa ba kaɗai ba.







A arewacin Najeriya, inda Karaye-Gari yake al'ada da addini suna cigaba da taka muhimmiyar rawa a sha'anin 'yancin mata. An samu cigaba sosai a 'yancin mata musamman wajen faɗaɗa tattalin arziƙinsu da samun damar yin ilimi da kuma yadda suke shiga a dama da su a al'amuran al'umma. Duk da wannan cigaban da aka samu, har yanzu akwai ƙalubale wajen sanya su cikin al'amuran shugabancin da jin ta bakinsu yayin a ɗaukar wata matsaya kan wani al'amari da ba su mukamai da kuma ba su damar bayar da irin tasu gudummawar a sha'anin al'umma.

A Karaye-Gari, ba a taƙaice damar samun 'yancin ilimin mata ba, watau ana karfafa musu gwiwa su shiga makaranta.Sai dai cewa har yanzu akwai adadi mai yawa na matan da aka cire ko suka bar makaranta a dalilin za a yi musu auren wuri da sauran dalilai kamar ƙarancn makarantun jeka ka dawo na mata a kusa da gazawar iyaye wajen ɗaukar nauyin karatun 'ya'yansu mata da makamanta haka. An yi amfani da tsarin cobweb domin a nitsa sosai wajen tantance haƙƙoƙinmata. Tsarin na so ya auna yanayin zamantakewa da tattalin arziƙi da kuma siyasa domin a gano abubuwan da ke kawo tarnaƙi ga cigaban mata a garin.






Ma'aunin Cobweb na tantance haƙƙin maza





Ma'aunin Cobweb Na Tantance Haƙƙin Mata

KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN KARAYE-GARI 2016


## JADAWALI AYYUKAN YAU DA KULLUN

Anyi amfani da jadawalin ayyukan yau da kullum domin tantance haƙƙoƙin mata a garin domin sanin nauyaye-nauyayen da ke kansu a cikin al'umma. Rukunin mutane daban-daban ne (maza/mata, samari da yan mata) sukayi tantancewar a cikin garin don sanin yadda suke tafiyar da lokutansu a ayyuka daban-daban. Jadawalin dake biye ya nuna cewa maza sunfi mata yawan ayyuka haka ma yara maza sun fi yan uwansu yanmata yawan ayyukan yi a cikin al'umma. Yara mazan kan tafi da shanu wajen kiwo, yawanci dukkan ayyukan dake buƙatar amfani da ƙarfi yara mazan ne keyi.

Jadawali Ayyukan Yau Da Kullun na Matan Karaye-Gar



Jadawali Ayyukan Yau Da Kullun na Mazan Karaye-Gari






Wajen Zaɓe Yayin Samar Da Kundin Cigaban Garin

KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN ƘARAYE-GARI 2016



Wajen ƙidaya yayin Samar da Kundin Cigaban Garin

## Take Haƙƙoƙin Ɗan Adam


Duba da Rijistar Haƙƙin Ɗan Adam, (Anyi amfani da rijistar haƙƙin ɗan adam wajen tantance haƙƙoƙin ɗan adam a cikin al'umma) an gano cewa ana takewa mutanen Karaye-Gari waɗannan haƙƙoƙin:

Haƙƙin Samun Abubuwan more Rayuwa
Haƙƙin Samun Kayayyakin Aiki
Haƙƙin Samun Ingantaccen Ilimi
Haƙƙin ingantacciyar lafiya

Waɗannan haƙƙoƙi nada alaƙa da matsalolin da suke damun wannan garin. Dangane da waɗannan matsalolin da ake takewa, al'ummar Karaye-Gari sun haƙiƙance cewa ana take musu haƙƙoƙin ababan more rayuwa kamarsu wutar lantarki da hanyoyin mota. Daɗin daɗawa kuma an tauye musu haƙƙin ingantacciyar lafiya a garin yadda zasu taimakawa mata masu juna biyu da ƙananan yara.


# Lissafin Haƙƙoƙin Karaye Gari

| Jihar /LRP | KANO | | | KARAMAR HUKUMA | KARAYE | | GARI | | KADEMI | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Rashin cancanta/ cancanta a samu (mata, yara, talakan da ba shi da fili ko rukunin jama'ar da aka gano) | Adadin waɗanda suka cancanci su samu a yankin da aka yi shirin | | Al'amari | Abubuwan da suka haddasa | Haƙƙoƙin da aka tauye | Kundin tsarin mulki | Adadin waɗanda suka cancanci su samu damar da suke neman haƙƙinsu a farkon fara shirin | | Waɗanda nauyin ya hau kansu | Sauran muhimman masu ruwa da tsaki |
| | Namiji | Mata | | | | | Namiji | Mata | | |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 10,000 | 12,000 | Rashin Kyakkyawar Hanyar mota da gadoji | Rashin Wakilci nagari | Haƙƙin samun ingantattun ababan more rayuwa | UDHR da Kundin Tsarin Mulkin ƙasa | 10,000 | 12,000 | Majalisar ƙaramar hukuma. Ma'aikatar ayyuka da gidaje. | Kungiyoyi masu zaman kansu Kamfanonin gine-gine. |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 10,000 | 12,000 | Karancin tsaftaceccen ruwan sha. | Rashin Wakilci nagari | Haƙƙin samun ingantacciyar lafiya da kayayyakin aiki | UDHR da Kundin Tsarin Mulkin ƙasa | 10,000 | 12,000 | Ma'aikatar Albarkatun Ruwa. Ma'aikatar Kananan Hukumomi | Kungiyoyi masu zaman kansu |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 10,000 | 12,000 | Karancin kayayyakin lafiya da ma'aikatan lafiya | Rashin sa ido wajen ƙaddamar da ayyuka | Haƙƙin samun ingantacciyar lafiya | UDHR da Kundin Tsarin Mulkin ƙasa | 10,000 | 12,000 | PHMB. Ma'aikatar Lafiya ta Jiha Majalisar Karamar Hukumar Karaye. | Kungiyoyi masu zaman kansu Sassan Majalisar Ɗinkin Duniya |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 10,000 | 12,000 | Ilimi: ƙarancin kayayyakin koyo da koyarwa da ƙarancin malamai | Rashin sa ido wajen ƙaddamar da ayyuka Rashin Wakilci nagari | Haƙƙin Samun Ingantaccen Ilimi . | UDHR da Kundin Tsarin Mulkin ƙasa | 10,000 | 12,000 | Ma'aikatar Ilimin Firamare da Bai ɗaya. Ma'ikatar Ilimi ta Jiha | Kungiyoyi masu zaman kansu Sassan Majalisar Ɗinkin Duniya |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 10,000 | 12,000 | Noma ( noman rani) | Rashin amfani da damarmakin da ake dasu (shirin noman rani) | Haƙƙin Samun Kayayyakin Aiki | Kundin Tsarin Mulkin ƙasa | 10,000 | 12,000 | Ma'aikatar noma ta Jiha | Ma'aikatar Noma ta Kasa |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 10,000 | 12,000 | Rashin aikin yi/sana'o'i/ mata/masu buƙata ta musamman | Rashin amfani da damarmakin da ake dasu (shirin noman rani) | | Kundin Tsarin Mulkin ƙasa | 10,000 | 12,000 | Ma'aikatar Yaɗa Labarai da Cigaban Matasa ta Jiha | Majalisar Karamar Hukuma. |








# KALUBALEN DA KE FUSKANTAR KARAYE-GARI ‘YAMMEDI A HALIN YANZU



# KALUBALEN DA KE FUSKANTAR KARAYE-GARI A HALIN YANZU

Kalubalen dake fuskatar Karaye-Gari a halin yanzu sun haɗa da rashin ababan more rayuwa kamar wutar lantarki, ilimi, lafiya da sauran kayayyakin more rayuwar da suke taimakawa al'umma wajen cigabansu. Makarantar firamaren ƙwalli ɗaya da ake da ita nada ƙarancin ajujuwa da ƙwararrun malamai, yanayin da ilimi ke ciki a wannan gari shi ke bada ƙarin haske kan yanayi da harkokin lafiya ke ciki a garin. Wannan gari na fuskantar yawan matsalar mutuwar mata masu juna biyu da ƙananan yara saboda matsalolin da ke akwai a harkokin da suka shafi lafiya. Yanayin da hanyoyin garin ke ciki yayi mutuƙar taka rawa wajen kawo tangarɗa a harkokin lafiya kuma yana buƙatar duba na tsanaki wajen shawo kan matsalolin lafiyar garin.

A lokutan damuna, rayuwa kanyi mutuƙar wahala a wannan gari, ba ko yaushe yara ke zuwa makaranta ba, marasa lafiya basa iya zuwa asibiti haka nan jama'a ba sa iya ɗaukan kayayyaki zuwa kasuwa saboda rashin kyawun hanyoyin garin musamman hanyar Rogo/Karaye zuwa Tofa wadda ta wuce cikin Karaye-Gari zuwa Kabo, Rimin-Gado da Tofa.

Akwai hanyar ruwa (Kogi) a Karaye-Gari wadda ke bayar da gudunmowa ƙorai da gaske wajen noman rani. Idan aka gina hanyar yadda ya kamata za a ci moriyarta wajen noman rani. Wannan zai rage matsalar rashin aikin yi da jama'ar wannan gari ke fuskanta. Haka kuma zai rage matsalolin zamantakewa na yau da kullun ya kuma bunƙasa yanayin rayuwa a wannan gari.




KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN ƘARAYE-GARI 2016

Masu Buƙata ta musamman basa cin moriyar duk abubuwan da suka shafi ilimi hakan na yi musu barazanar ƙorai da gaske wajen samun kyakkyawar rayuwa a gaba.

An jera matsalolin wannan garin ta hanyar tsarin matsalar da tafi ciwa al'umma tuwo a ƙwarya a sama (duba jadawalin dake tafe), jama'ar garin sun saka matsalar hanya a matsayin matsala ta farko da ake bukatar a fara magancewa. Al'ummar wannan gari suna da yaƙinin cewa samar da hanya zai haɓaka rayuwarsu kamar yadda matsalar da ta shafi lafiya (ƙarancin kayayyakin lafiya da ma'aikatan lafiya) ta zama matsala ta shida da ke mutukar tauye cigaban rayuwarsu. Rashin aikin yi musamman a gurin matasa, mata da masu buƙata ta musamman ita ce matsala ta uku dake ci musu tuwo a ƙwarya, matsalar ruwan sha tazo ta biyu. Ilimi na ɗaya daga cikin abubuwan da suke fuskantar matsaloli a garin. Al'umar wannan gari nada ra'ayin cewa samar da kyakykyawan tsarin noman rani a Karaye-Gari da sauran garuruwa maƙota zai mutuƙar ciyar da yankin gaba ya kuma haɓaka noma amfanin gonar da aka fi sayarwa mutuƙar dai akwai kyakykyawan shiri wanda zai taimakawa jama'ar yankin wajen noman rani.

## SASSAUKAR HANYAR JERA MATSALOLI

Domin faɗaɗa tantance matsalolin anyi amfani da sassaukar hanyar jeran matsaloli don samun matsaya kan yadda za a magance su



PAIR WISE RANKING OF

| ISSUES | WOMEN | CHILDREN | MEN | TOTAL | RANK |
|---|---|---|---|---|---|
| HEALTH General Hospital | 06 | 10 | 61 | 77 | 1st |
| EDUCATION – Additional class | 03 | 12 | 58 | 73 | 2nd |
| UNEMPLOYMENT | 00 | 08 | 55 | 63 | 3rd |
| DRUG ABUSE | 00 | 00 | 6 | 6 | 6th |
| WATER | 01 | 05 | 25 | 31 | 5th |
| ROAD | 21 | 05 | 15 | 41 | 4th |
| POOR NETWORK | 00 | 00 | 05 | 05 | 7th |

## SASSAUKAR HANYAR JERA MATSALOLI

| AL'AMAR (BUKATU)I | MATA | YARA | MAZA | ADADI | MATSAYI |
|---|---|---|---|---|---|
| LAFIYA | 06 | 10 | 66 | 11 | 1st |
| ILIMI | 03 | 12 | 58 | 73 | 2nd |
| RASHIN AIKINYI/ SANA'O'I | 00 | 08 | 55 | 63 | 3rd |
| SHAN MIYAGUN KWAYOYI | 00 | 00 | 06 | 06 | 6th |
| INGANTACCEN RUWAN SHA | 01 | 05 | 25 | 31 | 5th |
| HANYA | 21 | 05 | 15 | 41 | 4th |
| INGANTA WAYAR SADARWA NETWORK | 0 | 0 | 05 | 20 | 7th |







Wasu Daga Cikin Mahalarta Taron Samar Da Kundin Cigaban Karaye-Gari



# TANTANCE MATSALOLI TA AMFANI DA BISHIYAR MATSALOLI








Ita wannan bishiya na taimakawa wajen faiyace matsalolin al`umma da aka binchiko. Ita wannan bishiya tana nuna dangantakar waɗannan matsaloli da dalilan afkuwarsu da kuma illar da suke da ita idan ba a magance su ba. Don haka, kai tsaye za a tafi kan tushen matsalar domin magance matsalar gabaɗaya. Tushen matsalar jama'ar wannan gari shi ne ƙarancin hanya a cikin garin, ganyan bishiyar kuma shi yake nuni da abin da matsalar zata jawo idan ba a magantata ba. Ga dai yadda bishiyar matsalolin take.

Tushen matsalar wannan gari shi ne ƙarancin kwalbatoci da magudanar ruwa, zaizayar ƙasa, matsalar ingantaccen jagoranci nagari, hanyoyin da gwamnati ke ginawa ba ingantattu bane, rashin bibiyar ayyukan gwamnati, rashin ƙungiyoyin sa kai domin bibiyar shugabanni wajen samar da aikin cigaban gari a ƙarancin wakilci wajen samar da muradin ƙarni na cigaban al'umma (MDAs).

An bayyana dalilan da suka jawo waɗannan matsalolin kamar haka: ƙarancin himmar aiki, taɓarɓarewar tattalin arziƙi, yawaitar yaɗuwar cututtuka, wahalhalun rayuwa, ƙaruwar mutuwar mata masu juna biyu, ƙarancin bayanai da sadarwa da kuma rashin cigaban garin.

Dangani da waɗannan lammuran da suka taso daga bishiyar matsaloli a wannan gari, an yi nazarin ƙungiyoyi da mutanen da za su iya bayar da gudummawa wajen warware matsaloli. Al'ummar Karaye-Gari sun fitar da muhimman mutanen da suke da zarafin tallafawa domin samar da canjin da ake fata a garin.

# JADAWALIN TANTANCE MATSALOLIN KARAYE-GARI

| ABUBUWAN DA AKA GANO | WAƊANDA ZA SU IYA TALLAFAWA | CIBIYOYI | DALILAN BUKATU/ ZABURARWA DOMIN KAWO CANJI | MATAKIN KARFIN IKON KAWO CANJI |
|---|---|---|---|---|
| LAFIYA | 1. Mai Unguwa Da Dagaci.<br>2. Kansila<br>3. Shugaban Karamar Hukuma<br>4. Dan Majalisar Jiha<br>5. Dan Majalisar Tarayya<br>6. Gwamnan Jihar Kano<br>7. Sanata<br>8. Kwamishinan Lafiya<br>9. Masu Taimakawa Al'umma<br>10. Sakataran Ilimi<br>11. Kwamishinan Ilimi<br>12. SUBEB)<br>13. Mutanen Gari masu Tallafawa | Ma'aikatar Kasafin Kuɗi,<br>Ma'aikatar Kananan Hukumomi<br>NUT/SBMC<br>Karaye MicroFinance Bank, Majalisar ƙaramar hukumar Karaye,<br>Kwamitocin Ilimi, Lafiya da Samar da aiki, na Majalisar Jiha,<br>Ma'aikatar Ilimi da Hukumar makarantun sikandire (KSSSMB | Cigaba<br>Siyasa<br>Siyasa<br>Siyasa<br>Siyasa<br>Siyasa<br>Siyasa<br>Domincigabaalumma<br>Siyasa | 1.L<br>2.L<br>3.H<br>4.M<br>5.M<br>6.H<br>7.M<br>8.H<br>9.M<br>10.M<br>11.L<br>12.H<br>L |
| ILIMI | | | | |
| KARANCIN AIKINYI DA SANA'OI | | | Siyasa<br>Siyasa<br>Siyasa<br>Cigaba | |












## TANTANCE YANAYIN KARFIN IKO (NAZARI KAN WAƊANDA KEDA IKO)

An yi amfani da tsarin zane naƁenn domin gudanar da wannan tantancewar. Haka kuma anyi amfani da tsarin zanen Ɓenn domin tantance matakin ikon da wani mutum ko wata ƙungiyoyi ke da shi da kuma alaƙarsu da juna. Zanen dake tafe ya fitar da mutane da cibiyoyi waɗanda suke da ikon warware al'amari ko matsalar da aka gano. Sanan kuma zanen ya nuna tazarar da mutane da cibiyoyin suke daga garin da kuma alaƙar su da juna.



ƙarin Bayani: Zanen dake sama ya fitar da mutane da cibiyoyi waɗanda suke da ikon warware al'amari ko matsalar da aka gano. Sanan kuma zanen ya nuna tazarar da mutane da cibiyoyin suke daga garin da kuma alaƙar su da juna.

Shugaban ƙaramar hukumar Karaye da Ma'aikatar lafiya ƙarƙashin kwamishinan lafiya Kwamitin suna da tasiri wajen kawo gyara wajen daukaka asibitin Karaye da magance matsloloin laifiya agarin.Ɗan majalisa Jiha ƙarƙashin ko ta hanyar Kwamitin lafiya a majalisar jiha na da ruwa da tsaki wajen samar da kayan aiki kuma yana da tasirin maganta wadannan lammuran. Sanan kuma majalisar ƙaramar hukuma ita ma nada rawar takawa wajen sa lamarin gaba. Alaƙarta da ma'aikatar kasafin Kuɗi ta hannun ƙaramar hukuma kan sa maida hankali kan matsalar a duk matsalolin dake addabar al'ummar a wajen taron da masu zartarwa keyi duk mako.

Alaƙar da ake da ita tsakanin masu sarautun gargajiya, malaman addini da masu aikin gwamnati zasuyi mutuƙar taimakawa wajen magance wannan matsalar lafiya dama duk sauran buƙatun alummar ƙaraye. Masu muƙaman siyasa su ne gaba wajen yin magana da yawun al'umma, maganar da zata kawo canjin da ake buƙata a cikin al'umma. Haka kuma jama'ar garin sun zayyana sunayen wasu masu kishin garin waɗanda zasu iya taimakawa a sami canjin da ake buƙata.




TANTANCE HANYOYIN SAMUN BAYANAI

Karaye-Garina samaun bayanai daga waje ta hanyar zantuttukan al'umma, Jaridu, Rediyo, Talabishin, mai shela, GSM, yanar Gizo (Facebook da twitter).

Haka kuma suna musayar bayanai da mutane da cibiyoyi ta hanyar wasiƙa da kuma saƙunan baka.











# TSARIN DA AKA SHIRYA GUDANARWA NA AL`UMAR KARAYE-GARI

A ƙarshen tattaunawar, an fitar da ƙwaƙƙwaran tsarin da za a bi domin warware matsalolin da aka gano ta hanyar yinamfani da gudummawar kowa da kowa Da wasu dabaru domin tantance abubuwan da ke ci wa al'ummar Karaye-Gari tuwo a ƙwarya. Tsarin da ke biye tsari ne na ayyukan da za aiwatar domin ganin mafarkin garin ya zamagaskiya.


| MAHIMMAN BATUTUWA | AIKIN DA AKA TSARA GUDANARWA | WAƊANDA SUKA ƊAUKI NAUYI | KAYAN AIKIN DA AKE BUKATA | KAYAN AIKIN DA AKE BUKATA | MATSALOLI | SHAIDAR SAMUN NASARA |
|---|---|---|---|---|---|---|
| Rangadi don saduwa da sauran Jama`ar Karaye-Gari | Ganawar baka da baka | Yan Kwamitin Samar da Kundin Cigaban | Sati 3 zuwa 20 ga watan Janairu | Bayani game da wannan shiri | Kuɗi | Rahoto |
| Daftarin Cigaban Gari | Gabatarwa da amsar bayanai | CITAD/ Jami`in Gari | 27 ga watan Fabarairu | Bayanan Kundin cigaban gari, Mutane | Lokaci da Zirga-zirga | CITAD/ Jami`in Unguwa |
| Kaddamawar | Raba wasiƙun gaiyata | CITAD/ Jami`in Gari | 30 ga watan Afirilu | Sufuri Ganawa Ganawa da 'Yan Jarida | Samun mutane da ƙungiyiyin | Ranar ƙaddamarwa |
| Rangadi don saduwa da sauran Jama`a | Ziyarar gaisuwa da rokon iri | CITAD/ Jami`in Gari | Bayan Kaddamawar | CITAD/ Jami`in Unguwa Ganawa da yan jarida | Lokacin damuna da ayyukan Noma | Kaiwa da komowa rahoto |









# HOTUNAN DA AKAYI AMFANI DASU WAJEN SASSAUKAR HANYAR JERA MATSALOLI




ILIMI





Hanya




KARANCIN RUWAN SHA



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN KARAYE-GARI 2016




MIYAGUN KWAYOYI



NOMA



WAYOYIN SALULA (SADARWA)




LAFIYA